*Yobe Journal of Language, Literature And Culture Vol. 1*

# TARBIYYA GA RAYUWAR BAHAUSHE DAGA

Muhammad Rabiu Tahir
mrtahir@abu.edu.ng
07031340632
Sashen Harsuna da Al'adun Afrika
Jami'ar Ahmadu Bello, Zariya

*TSAKURE*

*Wannan mukala za ta yi bayanin ne, kan amfanin kyakkyawar dabi'a a rayuwar Bahaushe, domin rayuwa da dabi'a maikyau kusan a iya cewa kamar hanta cc da jinni, idan babu su kusan a iya samun matsala a harkokin rayuwa, ke nan sai da su rayuwa ki iya zarna kan tsari. domin haka kyakkyawar dabi'a kusan kowane mutum mai tsari na iya zama jami'inta domin nusarwa. Saboda haka wannan mukala za ta tattake bayani wajen fito da yadda kyakkyawar dabi'a ya kamata ta kasancc a rayuwa Bahaushe kamar zaman iyali da jagoranci wadanda ake gani kusan suna daga cikin ginshikan samar da mutum nagari wanda al'umma za ta yi tinlcaho da shi.*

## 1.1 GABATARAWA

Bahaushe mutum ne kamar yadda sauran halittun Allah suke, ko kuma a iya cewa Bahaushe da tarbiyya kamar hanta ce da jini wanda ba a iya raba su da juna. Kwatankwacin yadda jikin mutum yake buƙatar wasu abubuwan rayuwa domin samun inganci, haka tsarin rayuwar Bahaushe take buƙatar irin waɗannan abubuwa domin samun inganci da kuma daidaito.

Idan aka ɗauki Rai na mutum da Tunani da tarbiyya, kusan a iya cewa abubuwa ne, waɗanda ake iya amfana da su, idan sun sami tarbiyya ta shari'ar Allah gwargwadon hali, kuma a iya rasa hakan idan waɗannan abubuwa sun rasa wancan tsari na shari'a, domin tarbiyyar jikin mutum tana inganta ne da samun tattalin kayan gina ta ta hanyar ni'imar da ta dace da ita.

Bahaushe mutum ne wanda bai iya zama sai da tarbiyya, saboda ba zai zauna lafiya ba sai da tarbiyya. Wannan ya sa wasu masana ke ganin Mutum yana da rauni, wani ra'in na fahimtar Mutum yana da ruɗu. da irin wannan ɗabi'a ce wasu ke da tunanin cewa, ashe ba kowane mutum ne ke iya zama jami'in tarbiyya ba a cikin al'umma, sai wanda hankalinsa da tunaninsa da shekarunsa suka dace da tsarin tarbiyya ta asali.

Ko da yake duk da cewa Bahaushe wayayye ne, kuma yana son wayewa, sannan ga shi kuma yana son birnanci, wannan ya sa duk lokacin da ka hađu da shi za ka fahimci yana son birnanci. Domin Bahaushe mutum ne mai son riga mai kyau da hula mai kyau da abin hawa mai kyau kai har da kyakkyawar mace, komai mai kyau yake so ke nan wannan ya nuna Bahaushe yana da sha'awar abubuwa masu kyau.

A dalilin ya jawo ma kan sa abu mai kyau ne, yake da fushi. duk wanda zai kawo masa matsala kanabin da yake so ba za su daidaita ba, domin duk lokacin da ya miƙa hannu yana son wani abu, ba ruwan shi halas ne ko haram ne, shi dai buƙata ta biya ta kowane hali, ko kuma kowane yanayi.

Irin wannan hali ko yanayi kađai ya isa ya haifar da gaba da musifu a a tsakanin mutum da mutum. Kafin mutum ya zama wata ƙabila haka yake a đabi'ance, saboda haka kasancewar sa haka kađai ya isa ya haifar da ta shin hankali. ko husuma a tsakanin al'umma, idan haka mutum yake, mene ne zai iya warware wannan tunani na mutum a tsakaninsa da al'ummarsa?

Abin da zai iya magance ma Mutum wannan shi ne, shari'a daga mahalicci tare da masu kula da ita, domin su kafa shari'a da nuni yadda za a aiwatar, sannan su kare shari'a ko Mutum ya shiga taitayinsa, sai dai hakan bai hana idan mutum ya ga wani abu a wajen wani, kuma abin nan ya ba shi ƙaye ba laifi ba ne, kamar ka ga gidansa yana da kyau ka iya kalla ko abin hawa mai kyau, ka kalla ko wanin haka, sai dai idan ka miƙa hannu don ka đauki wannan abin sai a ce shari'a ta hana wannan, haka kawai ke iya sanya Mutum ya shiga taitayinsa, dangane da zamantakewarsa da mutum Đan uwansa da kuma zama lafiya kamar yadda shari'ar ta tanada.

## 2.1 TARBIYYA

Tarbiyya wani babban jigo ne ga rayuwar Bahaushe, idan babu tarbiyya a cikin tsarin rayuwar Mutum, lallai Mutum zai kasance kamar lokacin da ya fara rayuwa ta mai ƙarfi shi ne jari. Har ila yau ana buƙatar Mutum ya zauna lafiya. Idan ba haka ba, ba zai iya zama lafiya ba, sai an kafa masa shari'a mai tsari tare da masu gudanar da yadda ya dace abi tafarkin wannan shari'ar, domin wannan tsarin ke iya sanya kowane abu yadda ya dace, kuma a mazaunin da ya kamata ya zauna, sannan da kuma ba kowa haƙƙinsa gwargwadon hali. (Funtua, K.U. 1983)

A zamantakewar Mutum dangane da tarbiyya da shari'a ta mutum da mutum, aka kawo masa masu kare masa wannan tsari, sai aka kawo jami'ai domin su kare masa tsari da kuma Alƙalai, domin su tsare wannan tsari na shari'a, duk da haka wannan bai hana Gidan waƙafirashin cika ba, haka Gidan

waƙafi maƙil da Mutane, haka ya nuna ke nan Mutum ya keta shari'ar da Mutum ya shirya, wannan ya sa aka kai shi Gidan waƙafi, idan aka ƙyale shi sakaka ba za a taɓa zama lafiya ba, wannan ya nuna ke nan mutum kafin ya zama wata ƙabila haka yake, idan an kyale shi ba za a zauna lafiya ba. Domin wanda ma ya sana'anta shi ai ya bayyana shi da cewa mai yawan jahilci ne, kuma mai yawan zalinci ne, bisa wannan fahimtar ne wasu masana suke ganin hakan ya danganci ɗabi'a ta mutum da mutum a tsakaninsu da juna, duk abin da yake faruwa ga mutum kodai ya zama yana faruwa ne ga shi kansa, wanda hakan yana iya zama ɗabi'a, wadda a iya duban tata fuskoki kamar haka:

i Hikima
ii Kwazo
iii Kawaici

Dangane da waɗannan abubuwa da aka ambata a baya, mutum na buƙatar a yi masa kwaskwarima, dangane da haka, idan aka barsu ba tare da kwaskwarima ba, lallai Mutum ba zai zama mai kyau a ɗabi'a ba.

i **Hikima**: hikima dangane da mutum yana buƙatar daidaito, domin idan hikima ta yi yawa sai mutum ya riƙa ganin ya fi kowa, kuma ya riƙa raina kowa, haka kuma idan ta yi ƙasa sai ya zama wawa, saboda haka a wannan bagire ake buƙatar hikimar mutum ta zama ta yi daidai sai ya zauna lafiya da al'ummarsa.

ii **Kwazo**: a wannan yanayi ana buƙatar ƙwazon mutum ya zama ya yi daidai ko kuma tsaka-tsaki, idan ƙwazon mutum ya yi tsanani sai ya raina mutane da wulaƙantasu, ya dinga ganin sauran jama'a ragwaye, amma idan ƙwazo ya yi ƙasa da yawa sai mutum ya zama matsoraci mai rauni wanda ba zai iya tabbatar da komai ba, sai shirgidibagidi ko madalla tir.

iii **Kawaici**: idan Mutum ya zama ba shi da kawaici sai ya zama sha-sha, mai sha'awar duk abin da ya ga dama sai ya aikata. Idan kuwa kawaicin mutum ya zama ya tsananta sai ya zama ba shi da sha'awa, kuma ya zamo yana da macewar zuciya, ke nan ana buƙatar waɗannan abubuwa su kasance su na da daidato, dangane da Mutum da kuma kwaskwarima, tabbatar da haka zai taimaka gaya wajen ceto rayuwa daga shiga ruɗu. (Abdurrahman, N.S. 1999).

Saboda haka idan an yi la'akari da wannan bayani, kuma aka danganta shi da tsarin jikin mutum, wanda shi ma yana buƙatar daidaito da gyara. Komi na jikin Mutum idan ya saɓa da jikin za a ji ba daidai ba, a iya cewa yanayin jiki yanayin rayuwa, saboda idan tsarin jiki ya zama babu tsari za a sami akasi, haka tsarin rayuwa yake, ke nan idan ɗabi'a ta saɓa da tarbiyya, a iya samun

rashin daidaito a harkokin tafiyar da tsarin mutum, wannan yana haifar da kwaskwarima domin a ceto tarbiyya daga saɓanin da ta samu a tsakanin ta da ɗabi'a.

Wannan na iya zama wani misali da tsarin jiki wanda ya kamu da hawan jini, idan aka je wajen Likita babu wani magani da zai ba da, da ya wuce wanda zai sakko da jinin don ya zama daidai. Haka rayuwar mutum take dangane da ɗabi'a da kuma gangar jikinsa, wadda take buƙatar zama cikin tsari da daidai ko kuma tsaka-tsaki a kusan kowane lokaci, idan rayuwar mutum ta wuce tsari da daidaito zai ka mu da rashin lafiya, idan kuma daidaiton ya yi ƙasa zai kamu da rashin lafiya, da wannan a iya cewa rayuwar ɗan adam sai da gyara irin na shari'a, wanda shi ne maganin duk wani ciwon hawan jinin rayuwa.

## 2.2 Zaman Iyali

Wannan yana aukuwa ne a tsakanin Bahaushe da iyalinsa, dangane da gudanar da harkokin zamantakewarsu, idan wani abu ya faru a tsakanin Bahaushe da iyalinsa, ana buƙatar ya yi adalci. Haka ita ma ta yi adalci a tsakaninta da mai gidanta, ko kuma shi mai gidan ya yi adalci a tsakaninsa da danginta, ko kuma a tsakanisa da 'ya'yansa. Duk wani wanda za ka yi hulɗa da shi ana buƙatar adalci. Haka yana faruwa ne dangane da yadda Mutum yake, Saboda baya iya zama shi da wani a zauna lafiya, kusan dole sai an sami saɓani, walau daga iyali ko kuma makwabtaka a al'amuran yau da gobe.(Umar,M.B. 1987)

## 2.3 JAGORANCI

Shi ne tafiyar da harkokin al'umma abisa tsari na adala, da amintar da su daga tsoro da kalaci, in an yi haka an jagorantar gwargwadon hali. Duk wanda bai iya kiyaye kansa ba da ɗabi'unsa, ta yadda zai kiyaye iyalinsa su zauna lafiya ba. Mai irin wannan hali anya zai iya jagorancinal'umma wadda take ɗauke da jama'a iri-iri ga Barmo ga Chinedu ga Bulama da Ja'e da sauransu, kuma duk sun haɗa da mai hankali da mara hankali da masu rauni da masu ƙarfi, ta ina zai yi jagorancin wannan al'umma, haka ba zai samu ba sai ta hanyar jagoranci na shari'ar mai tsari. Ko da yake wanda yake da tsarkin zuciya da ƙaɗida ana fatan a same shi da cikakken hankali, kuma za a iya samun shi yana la'akari da abubuwan da ke faruwa, tun daga iyaye da kakanni har ya zuwa yau. (Ahmad, I. 1998).

Duk tarihin Duniya ba a taɓa samun wani Shuagaba da ya zo ya dauwama ba, idan lokacin sa ya wuce sai al'ummar da ya bari ta zo tana neman ya za ta yi ta zauna lafiya.Saboda babu tsarin shari'ar wannan shugaba

rashin daidaito a harkokin tafiyar da tsarin mutum, wannan yana haifar da kwaskwarima domin a ceto tarbiyya daga saɓanin da ta samu a tsakanin ta da ɗabi'a.

Wannan na iya zama wani misali da tsarin jiki wanda ya kamu da hawan jini, idan aka je wajen Likita babu wani magani da zai ba da, da ya wuce wanda zai sakko da jinin don ya zama daidai. Haka rayuwar mutum take dangane da ɗabi'a da kuma gangar jikinsa, wadda take buƙatar zama cikin tsari da daidai ko kuma tsaka-tsaki a kusan kowane lokaci, idan rayuwar mutum ta wuce tsari da daidaito zai ka mu da rashin lafiya, idan kuma daidaiton ya yi ƙasa zai kamu da rashin lafiya, da wannan a iya cewa rayuwar ɗan adam sai da gyara irin na shari'a, wanda shi ne maganin duk wani ciwon hawan jinin rayuwa.

## 2.2 Zaman Iyali

Wannan yana aukuwa ne a tsakanin Bahaushe da iyalinsa, dangane da gudanar da harkokin zamantakewarsu, idan wani abu ya faru a tsakanin Bahaushe da iyalinsa, ana buƙatar ya yi adalci. Haka ita ma ta yi adalci a tsakaninta da mai gidanta, ko kuma shi mai gidan ya yi adalci a tsakaninsa da danginta, ko kuma a tsakanisa da 'ya'yansa. Duk wani wanda za ka yi hulɗa da shi ana buƙatar adalci. Haka yana faruwa ne dangane da yadda Mutum yake, Saboda baya iya zama shi da wani a zauna lafiya, kusan dole sai an sami saɓani, walau daga iyali ko kuma makwabtaka a al'amuran yau da gobe.(Umar,M.B. 1987)

## 2.3 JAGORANCI

Shi ne tafiyar da harkokin al'umma abisa tsari na adala, da amintar da su daga tsoro da kalaci, in an yi haka an jagorantar gwargwadon hali. Duk wanda bai iya kiyaye kansa ba da ɗabi'unsa, ta yadda zai kiyaye iyalinsa su zauna lafiya ba. Mai irin wannan hali anya zai iya jagorancinal'umma wadda take ɗauke da jama'a iri-iri ga Barmo ga Chinedu ga Bulama da Ja'e da sauransu, kuma duk sun haɗa da mai hankali da mara hankali da masu rauni da masu ƙarfi, ta ina zai yi jagorancin wannan al'umma, haka ba zai samu ba sai ta hanyar jagoranci na shari'ar mai tsari. Ko da yake wanda yake da tsarkin zuciya da ƙaɗida ana fatan a same shi da cikakken hankali, kuma za a iya samun shi yana la'akari da abubuwan da ke faruwa, tun daga iyaye da kakanni har ya zuwa yau. (Ahmad, I. 1998).

Duk tarihin Duniya ba a taɓa samun wani Shuagaba da ya zo ya dauwama ba, idan lokacin sa ya wuce sai al'ummar da ya bari ta zo tana neman ya za ta yi ta zauna lafiya.Saboda babu tsarin shari'ar wannan shugaba

ta koma wurin mai ita, ko kuma babu waɗanda suka san wannantsari, hakan kusan yasa ya zama dole ga wannan al'umma ta nemi ya za a yi ta zauna lafiya, ke nan abin da shugabannin adala suka zo da shi, shi ne adalci cikakke, amma abin da manyan masana suka gano yana kama da adalci, sannan tsarin shari'ar mai kyau shi ne ke daidaita Mutum ya zama mai iya gudanar da jagoranci mai nagarta.(Ahmad. I. 1998).

Da wannan ne ake ganin Bahaushe a iya ɗora shi bi sa waɗannan matakai, ko ya iya aiwatar da jagoranci na adala, idan ya zama mai tarbiyya yana da kyau ya ɗanfaru da wasu matakai.

i Ya kasance ba shi da ƙawazucin abin da yake jagoranci.

ii Ya kasance ɗaya daga cikin jami'an tarbiyyar al'ummarsa

iii Ya kasance yana da sanin kusan komai na abin da zai je ya dawo.

iv Ya kasance yana iya ajiye komai yadda ya dace, ke nan ya zama yana da hikima ta ba kowa hakkinsa gwargwadon iko.

Dangane da waɗannan matakai, idan waɗannan matakai suka rasa wuri, ga mutum mai son jagoranci na adala, ba zai iya kafa komai ba sai ruɗu da harigido, akan haka wa zai iya kafa shugabanci wanda zai dace da al'umma ta wannan lokaci, sai dai a ce wanda ya sana'anta mutum kawai, abin nufi abu ne kusan mai wuya, mutum ya rasa waɗancan matakai, sannan a same shi yana adala a shugabanci.

Haka kuma abin da ya shafi, al'umma ko mutum shi ake kira ɗabi'a, wanda ake buƙata a sami hikima da kwazo da kawaici. Amma ya rasa wasu daga cikin muhimman abubuwan tarbiyya, kada hakan ya sa mutum ya yi tsammanin shi ne, mai iko ya yi zalunci domin yana da ƙarfi. idan ka zalunci iyali ko makwabci ko waninsu ai ba su suka haramta zalunci ba, aiwatar da haka ke haifar da rashin zama lafiya da tashin-tashina da sauransu.

Idan aka sami mutum yana da hikima da kwazo da kawaici, waɗanda za su taimaka masa ya ajiye komai daidai, da wannan a iya cewa sambarka domin ana fatan an sami matakan zaman lafiya a tsakaninsa da iyalinsa da makwabta da sauran al'umma. (Attahir. H.A. 2006).

## 2.4 KAMMALAWA

Bayani ya gabata dangane da yadda Mutum yake, da irin halayya ta mai rai da kuma yadda ya kamata Mutum ya ɗamfaru da shari'a mai tsafta, sannan an bayyana yadda Ɗan adam ke gwagwarmayar neman buyan buƙata ta kowane hali a dunƙule, sannan kuma da yadda shugabanci ya kamata ya zamo, tare da amfani da tsarin shari'a mai ɗorewa mai nagarta, ke nan Ɗan adam wani tsiro ne da yake buƙatar mani'imciyar ƙasa tare da samun

nagartaccen taki da kuma kulawa mai inganci gwargwadon iko. Ta haka ne Ɗan adam ke iya zama salin-alin ba tare da wata hayaniya ko rashin zaman lafiya ba. Amma duk waɗannan nan abubuwa sai jagorancin jagoran shari'a matabbaciya, ba jagorancin sha-sha-shu-da-sha-sha ba.

MANAZARTA


Abba, H.L. (1980) . Kunya Da Zumunta Tsakanin Hausawa. Kundin Digiri na Farko. Sashen Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero Kano.

Abdurrahman, N.S. (1999) *Taysiril Karimin Rahman Fi Tafsiri Kalamin Mannani* Dar al ibn Alhaishim Alqahir- Egypt.

Ahmad, I. (1998).*Tafsirin Sahih Muslim* ,Sautus-Sahaba Islamic Media Studio Production tare daAmincewar Darul-Hadith, Kano.

Attahir, H.A. (ed) (2006). *Jami' al Ulum wal Hikam*, Dar al Fajr, Cairo-Egypt.

Al-Bas'yuniy, H.A.[.(edit) (2006). *Jami'i Ulum wal Hikam,* Ibn Rajab, A.A. Egyft, dar alfajr Cairo.

Bugaje, U.M. (1991) The tradition of Tajdid in Western Bilad-al-sudan: a Study Genesis, Development and Pattern of Islam Revivalism in the Region 900-1900 A.D. Sudan: University of Khartoum, unpublished Ph.D thesis, p47-48.

Dikko, I. da Yawale, H.Z. (eds) (2010). *Tarjamar Ma'anonin Al}ur'ani Mai girma na Abubakar Mahmud Gumi (Suratul Mulk zuwa }arshe)* Nurul Islam Publishing House, Zaria.

Funtua, K.U. (1983) . Tarbiyya Da Dangoginta A Tsarin Zaman Hausawa. Kundin Digirin Na Farko, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero Kano.

Gumi, A.M. (1982): *Alkur'ani Mai Girma. Tarjamar Ma'anoninsa;* Dar al Arabia, Beirut, Lebanon.

Ibrahim, M.S. (1982) . Dangantakar Al'ada Da Addini, Unpublished M.A. Thesis, Department of Nigerian Languages, Bayero University, Kano.

Khalid, M.K. (1999) *Rijal Haula al-rasul.* 1st Ed. Beirut: Dar al-fikr. P.60.

Umar, M.B. (1987) . Tarbiyya A Bahaushiyar Al'da. Ma}alar da aka gabatar a babban taron ƙara wa juna Ilimi kan Harshe da Adabi da al'adu, Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.

nagartaccen taki da kuma kulawa mai inganci gwargwadon iko. Ta haka ne Ɗan adam ke iya zama salin-alin ba tare da wata hayaniya ko rashin zaman lafiya ba. Amma duk waɗannan nan abubuwa sai jagorancin jagoran shari'a matabbaciya, ba jagorancin sha-sha-shu-da-sha-sha ba.

MANAZARTA


Abba, H.L. (1980) . Kunya Da Zumunta Tsakanin Hausawa. Kundin Digiri na Farko. Sashen Harsunan Nijeriya Jami'ar Bayero Kano.

Abdurrahman, N.S. (1999) *Taysiril Karimin Rahman Fi Tafsiri Kalamin Mannani* Dar al ibn Alhaishim Alqahir- Egypt.

Ahmad, I. (1998).*Tafsirin Sahih Muslim* ,Sautus-Sahaba Islamic Media Studio Production tare daAmincewar Darul-Hadith, Kano.

Attahir, H.A. (ed) (2006). *Jami' al Ulum wal Hikam*, Dar al Fajr, Cairo-Egypt.

Al-Bas'yuniy, H.A.[.(edit) (2006). *Jami'i Ulum wal Hikam*, Ibn Rajab, A.A. Egyft, dar alfajr Cairo.

Bugaje, U.M. (1991) The tradition of Tajdid in Western Bilad-al-sudan: a Study Genesis, Development and Pattern of Islam Revivalism in the Region 900-1900 A.D. Sudan: University of Khartoum, unpublished Ph.D thesis, p47-48.

Dikko, I. da Yawale, H.Z. (eds) (2010). *Tarjamar Ma'anonin Al}ur'ani Mai girma na Abubakar Mahmud Gumi (Suratul Mulk zuwa }arshe)* Nurul Islam Publishing House, Zaria.

Funtua, K.U. (1983) . Tarbiyya Da Dangoginta A Tsarin Zaman Hausawa. Kundin Digirin Na Farko, Sashen Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero Kano.

Gumi, A.M. (1982): *Alkur'ani Mai Girma. Tarjamar Ma'anoninsa;* Dar al Arabia, Beirut, Lebanon.

Ibrahim, M.S. (1982) . Dangantakar Al'ada Da Addini, Unpublished M.A. Thesis, Department of Nigerian Languages, Bayero University, Kano.

Khalid, M.K. (1999) *Rijal Haula al-rasul.* 1st Ed. Beirut: Dar al-fikr. P.60.

Umar, M.B. (1987) . Tarbiyya A Bahaushiyar Al'da. Ma}alar da aka gabatar a babban taron ƙara wa juna Ilimi kan Harshe da Adabi da al'adu, Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, Jami'ar Bayero, Kano.